# Littafi mai Tsarki na yara

## Ke gabatar da

# Yesu ya Ciyar da Mutane 5000



**Wanda ya Rubuta: Edward Hughes**

**Mai Zane: Janie Forest**
**Alastair Paterson**

**Mai niyyan daukan nauyi: Ruth Klassen**

**Fassarawa: Bible Society Nigeria**

**Wanda ya Wallafa: Bible for Children**
**www.M1914.org**

**©2024 Bible for Children, Inc.**
**Zaku iya kofan wanna labarin ku wallafa idan**
**har ba zaku sayar da shi.**

Yawancin shugabanin addini (wanda ake kiransu Farisiyawa) sun fadi karya a kan Yesu. Wadansu ma sun yi kokari su kashe shi. Ba su ba da gaskiya cewa shi Dan Allah ne da gaske ba. Ba su karbe shi ba, ko da yake ya yi ayyukan ban mamaki wadanda suka nuna cewa Shi Dan Allah ne.



Wata rana, Yesu ya ketare Tekun Galili. Watakila yana so ya dan sha iska daga taron jama’a wadanda suke kewaye da shi kullum ne. Amma ba a dadde ba sai taron jama’ar suka gane inda yake. Sun sani Yesu ya aikata manyan ayyukan ban mamaki. Suna so su kasance tare da Shi.



Yesu ya bi da almajiransa zuwa wani wurin da ba kowa a tuddu inda ya zauna, yana koyarwa. Mutane sun yi ta zuwa a kai a kai. Ba a ddade ba sai lokacin abincin yamma ya yi. Babu shakka kowa yana jin yunwa.



**Yesu ya dubi taron jama’ar, “Ina ne za mu saya burodi domin mutanen nan su ci?” Ya tambaye Filibus. Babu shagon abinci a wurin. Mene ne Yesu yake shirin yi?**



**"Ai ba karamin kudi ba ne zai ciyar da mutanen nan," Filibus ya amsa wa Yesu.  Yesu da almajiransa ba su da isashen kudi.**





**Wani almajiri, Anderawus (dan’uwan Simiyon Bitrus) ya ce wa Yesu: “Akwai wani yaro a nan wanda yake da burodi biyar da kananan kifi biyu,…”**

**“…amma ina amfaninsu a cikin dumbun mutane kamar wannan?” Anderawus bai ga yadda wannan abincin dan yaron nan zai ciyar da mutane masu yawa kamar wadannan ba – ko da ma yaron yana da niyar ba wa Yesu abincin ranarsa.**



**Yesu ya ce, “Ku sa mutanen su zauna.” Sai mazan suka zauna a kasa, sun kai dubu biyar. Wow! DUBU BIYAR! Wannan ma ba a hadda da mata da yara ba, wadanda suke a wurin.**



**Biye da shi, sai Yesu ya dauki burodin da kifin. Babu shakka, dan yaron ya amince da Yesu. Bai san abinda ya sa Yesu yana son abincin ranarsa ba, ko kuma abin da Yesu zai yi da shi. Watakila ya yi tunani ya ce, "Idan na ba da abincin rana na, ba zan ci abinci ba." Amma duk da haka ya bayar da shi wa Yesu.**



**Sa’an nan, Yesu ya yi addu’a. Ya yi godiya ga Allah. A kan burodi biyar da kifi biyu? I’i! Yesu ya ce “Na gode maka” ga Allah ya kuma roke Allah ya albarkace abincin.**



**Bayan addu’a, Yesu ya kakkarya burodin da kifayen ya ba wa almajiran domin su raba wa taron jama’ar masu yawa. A lokacin ne mutane suka ga abin al’ajibin da Yesu ya yi. Kowanensu ya ci daidai yadda yake so. Amma duk da haka ba a iya cinye burodin da kifayen duka ba.**



**Bayan da aka ciyar da kowa, akwai gurasa da yawa da suka rage da kifi. “Ku tattara burbudin da suka rage domin kada a bar abu ya bata,” Yesu ya gaya wa Almajiransa. Suka cika kwanduna goma sha biyu na gurasan da abin da ya rage daga wadanda suka ci.**



**A ranar nan. Yesu ya ciyar da mutane fiye da dubu biyar (5000) da dan burodin abincin rana na wani yaro. Wani lokaci kuma, ya ciyar da mutane fiye da dubu (4000) da gurasa bakwai da ‘yan kifaye.**



**Sa’ad da mutanen da ana ganinsu ba kome ba suka ga wadannan alamu, ba su yi fushi kamar Farisiyawa ba. Maimakon haka sai suka ce, “Wannan shi ne Annabi na gaske wanda zai zo duniya.” Sun sani Yesu shi ne Mai Ceto wanda zuwansa aka yi alkawari ta wurin Kalma mai tsarki na Allah.**



# Yesu ya Ciyar da Mutane 5000

**Tahiri da ga maganar Allah, littafi mai Tsarki**

**a na samu a**

**Yohanna 6**

**“Shigowar maganar ka yana baduar kawo haske.” Zabura 119:130**

# KARSHE

51

60

**Wanan tahiri daga littafi mai-tsarki na mana bayanin Allah mu wanda ya halicce mu wanda yake son mu san shi.**

**Allah ya san da cewa mun yi abubuwan da ba su da kyau, wanda yake kira zunubi. Sakamakon zunubi mutuwa ne, amma Allah ya na kaunan mu sosai. Ya aiko da Ɗansa Yesu, ya mutu a kan giciye ya sha wahala domin zunuban mu. Kuma sai Yesu ya tashi daga matattu ya koma gida a sama. Idan ka bada gaskiya ga Yesu. Ka roƙeshi gafaran zunuban ka, zai yafe. Kuma zai zo ya zauna a cikin zuciyan ka kaima kuma zaka zauna a zuciyar shi har abada.**

**Idan ka yadda da wannan gaskiya ne, Ka cewa Allah:**
**Ya Yesu, na bada gaskiya kai Allah ne, ka kuma zamu mutum don ka mutu domin zunubi na, kuma yanzu ka tashi. Ina roƙon ka, ka shiga cikin zuciya na kuma ka yafe min zunubai na, Domin in samu sabon rai yanzu, kuma wata rana in zauna tare da kai har abada. Ka taimake ni in yi maka biyayya kuma in yi rayuwan da zai gamshe ka a matsayin ɗan ka. Amin.**

**Ka karanta littafi mai-tsarki kuma ka yi magana da Allah a kulla yaumin. Yahaya 3:16**